CRASH-3
Clinical Randomisation of an Antifibrinolytic in Significant Head Injury

# TAKAITACCEN BAYANI GA 'YAN UWAN MARAR LAFIYA

## GWAJIN CRASH-3

Tranexamic acid don magance raunin kwakwalwa mai tsanani; gwajin canke mai sarrafawar maganin gwaje na duniya baki daya

*Dan uwanka yana da rauni a kansa da ke bukatar kulawar gaggawa. Zai/za ta sami duk kulawar gaggawa ta raunin kai da muke bayarwa a wannan asibiti. Bayan haka kuma, za mu so mu hada da shi/ita a cikin wani nazari na duniya. Wannan nazari zai gano ko kwayar magani mai suna tranexamic acid tana rage zubar jinni a cikin kai bayan samun rauni a kai. Muna fatan cewa kwayar maganin zai yi dalilin samun kyakkyawar waraka. Mun san cewa kyayar maganin tana rage zubar jinni a sauran nau'o'in raunuka masu tsanani kuma ba tare da haifar da wasu matsaloli ba, amma har yanzu ba mu sani ba ko yana aiki a rauni na kai.*

*A matsayin bangaren nazarin, za a yi wa dan uwanka allura a jijiya da kuma Karin ruwa a cikin sa'o'i takwas. Za a baiwa rabin marasa lafiyar da ke cikin nazarin* tranexamic acid yayin da daya rabin za a ba su wata kwayar magani ta bogi (wani maganin ruwa da babu tranexamic acid a cikinsa). Sai a karshen nazarin ne za mu san waye ya sami wani nau'in magani. Za mu bukaci tattara wasu bayanai game da halin lafiyar dan uwanku don aikawa da su zuwa babban ofishinmu da ke Landan.

*Idan kana son karin bayani game da nazarinmu yanzu, to za mu gaya maka. Amma a madadin haka za mu yi maka Karin bayani daga bisani. Shin ka yarda mu fara bada maganin don nazari?*

**E, na yarda ku fara.**

Suna: ______________________________________

Sa-hannu: ______________________________________

Dangantaka da Marar lafiya: ______________________________

Kwanan wata: ______________________________________

*(Cike inda ake bukata kadai)*